**27 Ogusta, 2021**

(١)

**CIKA ALKAWARI DA SAKAYYA AKAN ABU MAI KYAU**

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Kada ku manta falala da take tsakaninku)** [al- Baƙra: 237]. Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai cika alƙawari, da gabatar da sakayya ga waɗanda suka kyautata mana yana cikin manyan ɗabi'un mutuntaka masu falala, ɗabi'un da addininmu mai girma da asali ya yi kira zuwa gare su, tabbas Allah Mai girma da ɗaukaka ya yabi Annabawa (Alaihimus Salam); sakamakon sun sifantu da wannan muhimmiyar ɗabi'a, Allah mabuwayin Sarki ya ambaci Sayyiduna Ibrahim (AlaiHis Salam) da cewa: **(Da Annabi Ibrahim (AlaiHis-Salãm) wanda ya kai matuƙa wajen cika alƙawarin da ya ɗauka wa Allah)** [an- Najmi: 37], game da Sayyiduna Yahya (AlaiHis Salam) kuma Allah mai girma da ɗaukaka ya ce: **(Mai tsananin biyayya ne ga mahaifansa biyu, ba fanɗararre mai saɓon Allah ba ne shi)** [Maryam: 14].

Lallai babu shakka kan cewa, waɗanda suka fi cancanta da a cika masu alƙawari, a kuma saka masu akan alhairan da

suka gabatar su ne iyaye biyu, su ne suke da cikakkiyar falala akan 'ya'yansu, lallai Allah Mabuwayi ya bayar da umurnin kyautata wa iyaye, da cika masu alƙawari, Allah mai girma yana cewa, yana tuna wa 'ya'ya irin ayyukan alhairai da iyaye suka yi masu, a lokacin da girma gami da rauni suka kama iyayen: **(Ubangijinka ya hukunta cewa kada a bauta wa kowa sai shi kaɗai, su kuma iyaye a kyautata masu.. Idan tsufa ta kama ɗaya daga cikinsu, ku dukansu su biyu, to kada ka soma ka yi tir da su, kada kuma ka kuskura ka hantare su, ka dai faɗa masu magana ta karamci.. Ka kwantar masu da kai cikin tausayawa, ka yi addu'a ka ce: Ya Ubangiji ka yi masu rahama kaman yanda suka raine ni tun ina ƙarami)** **[al- Isra'i: 23 -24]**, haka ma cika wa iyaye alƙawari, da yi masu kyakkyawar sakayya ba su tsaya kawai a sanda suke raye ba, har bayan watafinsu, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa**: (Lallai biyayyar da take sama da kowace biyayya ita ce zumuncin da ɗa yake yi da masoyan babansa).**

Haka ma a cikin mafi girman surorin cika alƙawari akwai: cika alƙawari tsakanin ma'aurata biyu, ta hanyar bayar haƙƙoƙin juna, da kuma kyautata rayuwar zamantakewar aure a tsakanin juna, da kuma kiyaye wa juna ayyukan alhairi da suka gudana a tsakaninsu, Allah Maɗaukakin sarki yana cewa: **(A cikin ayoyinsa ne –mai girma da ɗaukaka- ya halitta maku abokan zamanku daga cikinku, saboda ku sami sukuni da natsuwa a wurinsu, ya kuma sanya soyayya da tausayi a tsakaninku, lallai a cikin**

**wannan abu akwai ayoyi masu yawa ga mutanen da suke tunani)** **[ar- Rum: 21]**. Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Ku kyautata wa mata..).** Lallai duk wanda ya lura da rayuwar Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da kyau, zai irin yanda yanda (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya yi zarra wajen cika wa matarsa Sayyida Khadija (Allah ya ƙara yarda da ita) alƙawari, da kiyaye gudummuwar da ta ba shi wajen yaye masa damuwa, da taimakonsa da ta yi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), lallai Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya kiyaye mata waɗannan ayyukan alhairi da ta yi masa har bayan wafatinta, yana yawan ambaton alhairanta, yana yaba mata, da kuma nema mata gafarar Allah, yana kuma girmama ƙawayenta, wata rana wata tsohuwa ta zo wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), sai aka ga ya tashi, ya yi haba- haba da ita, ya girmama ta, sai Sayyida A'isha ta tambaye shi game da haka, sai ya ce mata: **(Tana zuwa mana lokacin Khadija na da rai, kuma kyautata cika alƙawari yana cikin imani).**

Haka ma a cikin surorin cika alƙawari akwai cika wa waɗanda da suke da falala akanmu alƙawari, wannan ya bayyana ƙarara a matakin da Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ɗauka; domin ya faranta ran mutanen Madina da suka taimaka masa (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), bayan ya rarraba ganimomi a ranar yaƙin Hunain, yana ce masu: **(.. Na rantse da wanda rayuwar**

**Muhammadu take hannunsa, ba domin hijira ba da na zama ɗaya daga cikin mutanen Madina "al- Ansar", da dukan mutane za su bi wata hanya, mutanen Madina "al-Ansar" kuma su bi wata hanya, da hanyar mutanen Madina zan bi. Ya Allah ka tausaya wa mutanen Madina, da 'ya'yan mutanen Madina, da jikokin mutanen Madina)**, haka ma game da su ne dai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Lallai mutanen Madina "al-Ansar" sun sauke nauyin da yake kansu, nauyin da yake kanku ne ya yi saura; saboda haka ku kyautata wa masu kyautatawa a cikinsu, ku kuma yafe wa wanda ya yi ba daidai ba a cikinsu)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yakan yi magana game da Sayyiduna Abubakar (Allah ya ƙara yarda da shi) yana cewa: **(Lallai wanda ya fi falala a kaina wajen abokantakarsa da dukiyarsa shi ne Abubakar).**

Hasali ma ita ɗabi'ar cika alƙawari tare da waɗanda suke da falalar gabatar mana da alhairi tana da faɗin da har ta haɗa da waɗanda ake da saɓani da su, dole ne mu kiyaye masu ayyukan alhairin da suka yi mana, mu kuma saka masu akan haka, za mu ga haka a fili lokacin da Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya tuna da al-Muɗa'im Bn Addiyyu, wannan mutumin da ya shigar da Annabi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) garin Makka ƙarƙashin kulawarsa, bayan ya dawo daga tafiyar da ya yi zuwa garin Ɗa'if, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Da a ce al- Muɗ'im Bn Addiyyu yana**

**raye, ya kuma yi mini magana game da waɗannan, da na miƙa masa su)**, yana nufin: fursunonin yaƙin Badar.

Haka ma a cikin surorin kiyaye alƙawari da cika shi akwai: ciwa wa malamai alƙawari ta hanyar girmama su, da yi masu ladabin da ya dace da su, da yi masu addu'a, Imam Abuhanifa (Allah ya ƙara yi masa rahama) yana cewa: tun sanda malami na Hammad ya rasu, ban taɓa yin sallah ba face na nema masa gafara shi da iyaye na, lallai ina nema wa malamai na da suka karantar da ni gafara, da ma waɗanda na karantar da su. Imam Ahmad (Allah ya ƙara yi masa rahama) yana cewa: Shekaru talatin da suka wuce ban taɓa kwana ba tare da na yi wa Imam al- Shafi'iy addu'a, na nema masa gafara ba.

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Lallai a cikin mafi girman cika alƙawari, da kuma gabatar da sakayya ga waɗanda suka kyautata akwai: kishin ƙasa, babu shakka hakan yana cikin cikan mutunci da girman ɗabi'a, al- Asma'iy (Allah ya ƙara masa rahama) yana cewa: Idan kana son ka gane cika alƙawarin mutum, to ka dubi irin yanda yake kallon makusantansa, da kishin da yake yi wa ƙasarsa, da begen da yake yi wa 'yan uwansa, lallai za mu

iya ganin wannan ɗabi'ar a fili a cikin rayuwar Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), a daren da zai yi hijira ne ya tsaya ya kalli garin Makka, bayan mutanen garin sun cutar da shi, sun kuma cutar da sahabbansa, sun kuma ƙaryata shi, sai ya ce: **(Lallai ke ce garin Allah da na fi so, ba domin mutanenki sun fitar da ni ba da ban fita ba)**, haka ma lokacin da zai yi wa garin Madina addu'a cewa ya yi: **(Ya Allah Ubangiji ka sanya mana soyayyar Madina, kaman yanda muke son Makka, ko sama da haka).**

Lallai muna matuƙar buƙatar mu yi ado da ɗabi'ar cika alƙawari, da saka wa waɗanda suka gabatar mana da alhairai, domin wannan ɗabi'a ce mai girma, tana ɗaukaka darajar mai ita, imani kuma yana cika, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Zaɓaɓɓun cikinku su ne masu cika alƙawari, masu sauƙi wajen mu'amala)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai mai cikakken imani a cikin muminai shi ne wanda ya fi kyawawan ɗabi'u).**

**Ya Allah Ubangijinmu ka shiryatar da mu zuwa ga kyawawan ɗabi'u, ka kuma kiyaye mana ƙasashenmu baki ɗaya.**